# MAI DA RUWA RIJIYA BA VARNA BA CE

Ibrahim Najahu Kumbashi
Department of Hausa
Federal University of Education, Kontagora, Niger State
najahukumbashi@yahoo.com
08020533197

&

Suleiman Abdullahi Wamba

Department of Hausa
Federal University of Education, Kontagora, Niger State
sulewamba71@gmail.com
08064465752

DOI: https://doi.org/10.5281/zenodo.14647540

**Abstract**

*The method of teaching L1 and L2 cannot be overemphasized. Therefore, this paper tries to x-ray the methodology of teaching Hausa L1 and L2 and how this method could deal with two situations in a classroom environment. It also touches some aspect of pronunciation and how the accent it an individual interfaces with L2. It goes further to proffer solution on how this problems can be minimize to a bearable level. The use of minimal pairs stress and intonation work are also discussed.*

Key words: Harshe, L1, L2, Manhaja, Tsarin shirin batutuwa.

## 1.0 Gabatarwa

Harshe na xaya (L1) shi ne harshen da mutum ya tashi a cikin shi. Harshen uwa ko kuma harshen da aka haifi mutum a cikinsa ko kuma harshen gado. Yanayin harshe na xaya ko kuma harshen uwa ko na gado da buqatun koyar da shi ya bambanta tsakanin harshe xaya da harshe na biyu. Mai koyon harshe na xaya da ma yana da shimfixa wadda ba ta bambanta

ONLINE ISSN: 2756-5599

sosai ba da abin da za a koyar da shi a cikin manhaja. Abin da zai koya nau'i xaya ne da abin da ya saba yi. Saboda haka zai koyi nahawun harshe ne, da hanyoyin sarrafa shi da faxaxa shi. Sannin kanmu ne cewa harshe na xaya ne ya tashi da shi (yaro), kuma ya tashi a cikin sa, kuma da wannan harshen ne ya buxe baki ya fara koyon furta baqaqe da koyon furta magana. Wato ban da wannan harshe, bai fara mu'amala da wani harshe na daban ba. Wannan harshe da ya tashi a cikinsa ne ya ji iyayensa na magana a tsakaninsu. Dangane da waxannan dalilai ne ya sa akwai buqatar koyar da shi domin yaro ya qalailaice harshe ta fuskar al'ada da adabi da nahawu.

Bayan wannan, kuma akwai qwarewa ta hanyar rubutu. Bugu da qari ana so a ga yara sun sami ginshiqi na qwarai da kuma gwanancewa sosai cikin harshen da yadda za sa samu qwaxayin zurfafa iliminsu a harshen domin qara faxaxa shi. Bayan wannan, buqatar koyar da harshe na xaya shi ne domin yara su nuna matuqar sha'awa da qauna da alfahari da harshen kodayaushe, kuma ko a ina musamman wajen rubuce-rubucen da aka wallafa a cikin harshen Hausa. Sa'annan kuma su bayar da gudummuwarsu a cikin qasidu da mujallu da jaridu da rubuce-rubuce a shafukan intanet da gidajen rediyo da gidajen telabijin. Su kuma samu qwaxayin sauraron shirye-shiryen Hausa a gidajen watsa labarai.

A taqaice, qwaxayin koyar da harshe na xaya shi ne domin yara su riqa bayyana kansu dalla-dalla a cikin al'ummar da suke, ko a wata al'umma ta gari.

## 1.2 Manhajar Harshe na Xaya A Makarantun Firamare

Manhaja tsarin kundin ilimi ne da hukumar ilimi ta qasa ta shirya ta bayar domin a yi amfani da shi a makarantun tarayya na qasa. Galibi akan shirya manhaja na wani lokaci mai tsawo. A qalla shekara huxu zuwa goma. Manufa ta cikin manhaja a xunqule take. Aikin malami na farko shi ne fassara manufar ta cikin manhaja domin a samu abin kamawa (Zarruq, 1979).

Manhajar harshen Hausa (L1) na xauke ne da manufofi da ake son yaran Hausawa su cimma cikin wani ayyananen lokaci. Wannan lokacin kuwa tun da yaran firamare ne bai kasa shekara shida (6). Daga cikin manufofin na cikin manhaja ta hukuma akwai:

- Koyar da Hausar baka
- Koyar da karatu
- Koyar da rubutu
- Koyar da al'adun Hausawa
- Koyar da adabin Hausawa
- Koyar da Nahawu

Fassarar waxannan manufofi na cikin manhaja da hukumar ma 'aikatar ilimi ta bayar ta ce a bi shi ne aikin farko da malami zai yi. Idan har ya fassara, sai ya shirya tsarin shirin darasi na rana-rana. A taqaice ga yadda tsarin yake:

Manhaja (Syllabus)

↓

Tsarin shirin mako-mako (Scheme of work)

↓

Tsarin shirin batutuwa (Units plan)

↓

Tsarin shirin rana-rana (Lesson plan)

Wannan shi ne hanyar fassara manufa ta hukama da malami zai bi domin ya cimma tashi manufar. Ana koya wa mai harshe waxannan fannoni ne na harshe domin ya naqalci tsarin harshe da sanin hanyoyin sarrafa harshen da faxaxa shi.

Idan malami na koyar da harshen Hausa ga haifaffen harshen ya kamata a kodayaushe ya ya tabbatar da ya san yaran da yake mu'amala ta koyarwa da su. Wannan sanin zai danganci sanin al'adunsu da qwazonsu da hazaqarsu da shekarunsu da kuma muhallin hulxar ta koyarwa. Hakazalika ya kamata malami mai koyar da harshe ya san:

- Matsayin yaran a cikin harshe
- Ra'ayin yaran dangane da harshe
- Ya yi la'akari da kayyakin aikin koyo da koyarwa. Dai dai sauransu.

Da zaran malami ya gamsu, sai ya tsara jadawalin yadda zai tafiyar da aikinsa. Domin mafi yawa a wannan qasa ana iya samun xalibai a cikin halaye biyu:

- Ana iya samun xalibai da asalinsu ba Hauswaa ba ne, amma suna zaune ne a qasar Hausa.
- Ko kuma malami ya samu kansa a ajin da yara ke qasar Hausa kuma su Hausawa ne.

Idan malamai ya samu kansa a irin halin da ake haxe masu magana a matsayin L1 da L2 sai ya riqa koyarwa ta hanyar karkasa su qungiya-qungiya, ko rukuni-rukuni. Yin haka zai sa kowane yaro ya samu wakilci a cikin aji ko a muhallin koyo da koyarwa.

Akan samu yanayin da yaran na Hausawa ne amma ba su iya Hausar ba kamar waxanda aka haifa kudu ta yamma (qasar Yarbawa) sai kudu ta kudu (qasar Ijaw) da kudu ta gabas (qasar Igbo). Malami zai yi amfani da wannan salo na koyarwa:

- Ya fara koya masu abin da suka sani, sannan zuwa ga abin da ba su sani ba. Malami zai yi amfani da matallafa koyo da koyarwa.
- Ya riqa koyarwa da nuna misalai a aikace.
- Malami ya riqa furta kalmomi cikin natsuwa, sannan ya umurci xalibansa su maimaita bayan shi.

A wannan fannin, malami zai yi amfani da dabarar koyarwa irin wannan:

- Kawo kalmomi da yadda ake furta su.
- Koyar da sauqaqqun jumlolin Hausa. A nan malami ya lura da nahawun jumlolin.
- Yawaita sa su hira da muhawara a tsakaninsu a cikin harshen Hausa (FME/NTI Kaduna, 2016).

**2.1 Koyar da Hausa A Matsayin Harshe na Biyu (L2)**

Harshe na biyu harshe ne da mutum ya koya baicin wanda ya koya gida ko ya gada daga iyayensa ko kuma ya tashi cikinsa. Wani lokaci kuma ana kiransa da baqon harshe. Baqon harshe na iya kasancewa na cikin gida ta fuskar maqwabtan Hausawa na kusa. Akwai kuma baqon harshe da Bahaushe ya ci karo da shi ta hanyar mu'amalarsa da baqi na nesa. Misalin waxannan maqwabtakan Hausawa na nesa sun haxa da Asiyawa da Azibinawa da Larabawa da Turawa da sauransu. Mu'amalar da Bahaushe ya yi da waxannan baqi ta addini ko mu'amala ta ilimi ko mu'amala ta kasuwanci sun haifar da samuwar harshe na biyu (L2) a qasar Hausa (Kusharki, 2004)[1].

Daga cikin harsunan da suka samu karvuwa suka yi tagomashi a idon Bahaushe su ne, harshen Faransa da harshen Ingilishi da harshen Larabci. Doguwar mu'amala ta Bahaushe da waxannan harsuna ta sa ya xauke su, kuma ya mayar da su harsunan da zai koya a matsayin harshe na biyu (L2) a makarantunsa. Wannan ya sa an samar masu gurbi a manhaja (syllabus) na makarantunmu na qasa.

**2.2 Hanyoyin Koyon Harshe Na Biyu (L2)**

[1] Lecture note, COE Minna.

Hanyoyin koyon harshe na biyu sun bambanta da na mai koyon harshe na xaya (L1). Ba ma mai koyo kawai ba, har da mai koyarwa. Domin mu'amalar koyo da koyarwa hulxa ce ta mutane biyu. Wato malami mai koyarwa da xalibi mai koyo. Akwai abu na uku da ake hulxa da shi, shi ne saqo wato abin da za a koya (Zarruq, 1979).

Mai koyon harshe na xaya (L1) yana da shimfixa wadda ta bambanta da abin da za a gabatar da xorawa a kansa. Abin nufi a nan abin da zai koya iri xaya ne da wanda ya riga ya iya, ya sani ya saba da shi ya kuma yarda da shi. Saboda haka zai koyi tsarin harshe ne da hanyoyin sarrafa shi da faxaxa shi. Shi ko mai koyon harshe na biyu (L2) ya zo ne tare da wani harshe cikakke, kuma iri daban da wanda za a koya mashi. Saboda haka a wurin wannan koyon harshen na biyu (L2) sabo ne a gare shi. Idan ba a zavi hanyar da ta dace ba, harshensa na asali yana iya zama tarnaqi ga koyon harshe na biyu.

A halin yanzu, muna da dabarun koyar da baqin harsuna da dama. Ana iya kasa waxannan dabaru gida biyu:

**2.2.1 Kashi na farko**: Na gargajiya. A nan, ana maganar waxanda aka gada tun kafin ilimin kimiyya da fasaha ya yawaita a qasar Hausa.

- Hanyar fassarar nahawu
- Hanyar koyi da kanka
- Hanyar doshe
- Hanyar takara a nahawu

Waxannan hanyoyi an same su ne tun kafin ilimin kimiyya da fasaha ya yawaita a qasar Hausa.

**2.2.2 Kashi na biyu: Na zamani**: Da ilimin kimiyya da fasaha ya yi yawa a qasar Hausa sai aka samu sabon tsari na koyarwa ta hanyar amfani da na'urorin zamani. Wannan yasa aka kasa waxannan matakan koyarwa na zamani gida uku.

i. Waxanda ake gani kawai. Waxannan nau'o'i na matallafa koyo ganin su kawai ake yi. Misali:

- Hotunan shuwagabanni
- Hotunan dabbobi
- Hotunan tsuntsaye
- Hotunan taswirori da asauransu

ii. Waxanda jin su kawai ake. Misali :

- Rediyo
- Rikoda ta hanyar amfani da kaset
- Garmaho ta hanyar amfani da faifai irin nasa
- Tangaraho

iii. Nau'i matallafa koyo da koyarwa na wannan kashi, matallafa koyo da koyarwa ne da ake ganin su kuma a ji su. Misali:

- Talabijin
- Bidiyo
- Majigi
- Komfuta
- Manya manyan wayoyin hannu da sauransu.

Waxannan hanyoyin koyo da koyarwa ne da aka samu ta hanyar vullowar kimiyya da fasaha a qasar Hausa.

**2.2.1a Hanyar Fassarar Nahawu**

Wannan ita ce tafi kowace salon koyarwa daxewa a cikin dabarun koyarwa. Wato a fagen koyar da baqon harshe. Ita ce hanyar da ake koyar da Larabci a makarantun zaure a qasar Hausa. Ma'ana hanyar koyar da baqon harshe bisa jagorar nahawu da taimakon Qamus ko fassarar malami. A ra'ayin masu bin wannan hanyar duk wanda ya haddace qa'idojin nahawu lallai ne ya mallaki harshe.

Matakan koyarwa: Mataki da ake bi a wannan hanyar shi ne a haddace muhimman qa'idojin nahawu. Misali, in ana son mai koyon Hausa ya iya fassara wakilan suna shuxaxxu da masu ci da masu zuwa kowani waxannan, sai a tsara su a cikin jadawali.

**2.2.1b Hanyar Koyi da Kanka**

Hanyar koyi da kanka `ya`uwar hanyar fassarar nahawu ce. Hanya ce ta rubutu da fassara da kuma gyara wa kai kurakurai.

Harshen da ake koyarwa ta wannan hanyar, ana xunqule shi a cikin littafi ne, kowane babi akan tsara shi mataki-mataki kamar haka:

- Bayanin nahawu a harshen mai koyo.
- Jerin sababbin kalmomi da ma'anoninsu
- Misalin jimloli da maganganu a harshen, don a fassara su zuwa harshen mai koyo.
- Misalin jumloli da maganganu a harshen mai koyo don ya fassara su zuwa harshe na biyu (L2)

Daga qarshen littafin akwai amsoshin domin gyara ayyukan da aka bayar a kowane babi. Duk lokacin da mai koyo ya aikata su yana iya buxo amsoshin don gyara aikinsa. Akwai jerin littattafai na koyi da kanka.

- Teach Yourself Hausa
- Jumlolin Hausa a sauqaqe (Hausa Simple Sentences)

- Jerin cikakken kwas domin sabon shiga (Complete Course for Beginners Series)

**2.2.1c Ingancin Hanyar Koyi da Kanka da Aibin ta**

Dabarun farko, idan aka dogara da littafin fassara da makarantu hawa-hawa, ingancinsu da aibinsu duk xaya ne da hanyar fassarar nahawu. Dayake hanyar koyi da kanka, na sa kai ne, ana sa ran za ta sa mai koyo ya yi himma da qwazo da kuma naci (Kusharki,2004). Dabarun da ke tare da fayafayen garmaho ko kaset kuwa, mai koyo zai ji muryar masu harshe ne tankar yana magana da su ne ido da ido. Daga cikin aibinsa kuwa, zai karanta harshen kai tsaye ba tare da fassara ba. Aikin nan na sauraro da karatu duk a baqon harshe ya isa tara hankalin mai koyo wuri xaya, kuma ya hana shi komawa.

**2.2.1d Hanyar Taqara A Nahawu**

Aikin taqara ne na iya magana ta amfani da sassan jiki. Mai koyo da koyarwa na amfani da sassan jiki ta gina kalmomin da mai koyan harshe na biyu (L2) zai dogara a kan su wajen koyon harshe. Baya ga waxannan abubuwa da za su jagoranci koyon harshe, akwai amfani da faxa da baka shi ne gaba da komai. Faxa da baka na gaba da karatu da rubutu. Wannan shi ne dalilin yin taqara musamman a darussan farko kuma a gabanin kowane darasin karatu da na rubutu.

Ayyukan taqara ana yin su ne akan wasu siffofin nahawu na harshe. Ana son mai koyo ya naqalce su ba tare da sai ya san sunayensu ba. Kuma ana zaven siffofin ne daga waxanda ke da alamar baqunta ga mai koyo. Bayan haka, ana tsamo su ne tare da jumloli ko maganganu masu ma’ana. In ma akwai lokaci ya kamata a fara da saurarar wani xan labari ko taxi ko wasan kwaikwayo. Daga nan sai a maimaita sassan da ake so mai koyo ya yi la’akari da su a hankali. Sai kuma a zavi wasu jumloli a yi taqara a kansu.

**Ire-Iren Taqara**

Ana iya rarraba taqara dangane da irin aikin da ake buqata wajen mai koyo. A kan yi magana mai koyo ya yi kwaikwayo, wato ya maimaita. A wata taqara kuwa amsa ne zai bayar, ko madadin maganar da aka yi ne. Ko ya harhaxa ta, ko ya cikasa ta ko kuma ya faxaxa ta. Ga wasu daga ire-iren taqara:

- Mai mai
- Tambaya da amsa
- Musaya
- Rikixarwa
- Xinki ko jerawa.

Waxanan su ne nau'o'in taqara ga mai koyon harshe na biyu (L2) zai ci karo da su a lokacin da yake koyon harshensa na asali don neman fassara.

Babban aibin wannan hanya kuwa shi ne rashin sanin sakamako. Da wuya a san yawan mutane da suka koyi harshe ta wannan hanya. Sannan da wuya a gane matsalolin hanyar kai tsaye, tun da masu koyo na cin gashin kan su ne. Ba su da wanda za su tunkara akan matsalolin koyonsu (FME/NTI, 2016 SDG).

**2.2.1e Hanyar Doshe**

Wannan ita ce dabarar koyon baqon harshe ba tare da fassara ko tahinta ba. A wannan hanyar, ana amfani ne da dabarar kwaikwayon mai baqon harshen. Baqon harshen da ya shigo wata qasa zai zama jigo ga waxanda ke da sha'awar koyon harshensa. Wannan zai

samu ne ta hanyar kwaikwayo. Ta wannan fasahar ne zai koyi harshe mutanen da ya baqunta su ma su koyi nasa harshen. A nan yana koyon harshen ne ta hanyar:

- Saduwa da abubuwa ko halaye waxanda suka wajaba ya bayyana su.
- Lura da irin yadda suke furta saututtukan da ke fitowa daga bakunan masu harshe.
- Kwaikwayon abin da masu harshen suke faxa akan nau'o'in da ire-iren kayayyakinsu.
- Yawan amfani da harshen a ko'ina, kuma a kowane lokaci.

**Matakan Koyarwa**

Abubuwan nan da aka misalta, waxanda mutum yakan yi idan baqon harshe ya zama masa lalura, su ake kwaikwaya wajen tsara hanyar doshe. Saboda haka, mataki na farko shi ne a sadar da xalibi da abubuwa ko halaye ko ayyuka waxanda za su yi jagora a koyon harshe. Ta hanyar nuni da kwaiwayo da misaltawa, za a gwada wa xalibi yadda zai ambaci kansa da abokan maganarsa duk a baqon harshe.

Mataki na biyu shi ne a shigar da xalibi halin da zai gabaci dukkan abubuwan da suka zama lalura a kansa.

**3.0 Shawarwarin da za su yi jagora**

Babban matakin inganta koyar da harshe ga xalibai duka masu harshen da ma baqon harshen ya dogara ga masana ilimin harsuna na gida da kuma harsuna na waje. Aikin waxannan masanan ne su shirya jadawali da tsarin shirin ilimi na qasa su tabbatar da ganin cewa ilimin harsunan gida sun samu qima a cikin manhaja ta qasa. Domin qwarewa ga ilimin harsuna na cikin gida zai kawo sauqi ga baqon harshe da ke sha'awar koyon harsunan na gida.

Masu shirya tsarin manhaja, su tabbatar da ganin cewa harsunan sun zama dole ga duk xalibanmu na firamare da kuma na sakandare. Tilasta koyon waxannan harsunan ne zai sa su samu tagomashi a nan cikin gida da waje.

Manhajar qasa ta tilasta wa hukumar shirya jarabawa ganin cewa kowane xalibi ya shigar da harshen yankin da yake a cikin jarabawar da zai rubuta a qarshen karatunsa na sakandare.

A sa shi dole cewa duk xalibin da ya gama sakandare in har zai shiga makarantar gaba da sai ya yi xaya daga cikin harsunan gida. In kuma yana koyon harshen don lalurar da zai ziyarci qasar da ake amfani da shi ne, sai ya koyi maganganu iri-iri na lalura. Kamar neman abinci da kwatancen wurare, kamar masauki da kasuwa da wurin ibada. Wannan na da muhimmmanci ga mai koyon harshe na biyu (L2).

Malaman koyar da harshe na da muhimmin rawa da za su taka wajen ganin sun samu karvuwa da tagomashi ga masu koyo. Za su yi haka ne ta qirqira da zaqulo misalai daga kyawawan al'adun da suka shuxe.

Harshe da al'ada da adabin al'umma da yawa na tafya kafaxa ne da junansu. Akwai al'adu da yawa na al'umma da ake samu cikin adabin waxannan al'umma. Waxannan sun haxa da matakan rayuwarsu. Matakan rayuwar sun haxa da haihuwa da aure da mutuwa da abincin da suke ci da kunya da yanayin kishinsu. Aiki ne na malamin koyar da harshe ya fito da al'adun nan da ke cikin adabi domin su samu sha'awan harshen.

Yana da muhimmanci ga xaliban koyon harshe da su jivinci sauraron kafafen yaxa labarai da kuma tattauna da kuma mahawara a tsakaninsu domin naqaltar harshen da suke koyo.

A taqaice, ya kamata hukuma ta taka rawa, na ganin duk wani da ya shigo gida Nijeriya ya xauki harshen vangaren da yake karatu ya koya na tsawon shekara xaya. Wannan tsari kar ya tsaya ga baqi kaxai, har da `yan gida maqwabtar juna.

**3.0 Kammalawa**

Harshe na xaya (L1) da harshe na biyu (L2) harsuna ne da mahaja ta tsara su ta kuma shirya su domin koyar da su a cikin gida. Hukuma ta shirya yin wannan ne domin a samu sauqin mu’amala da juna a cikin gida.

Bayan wannan kuma, Nijeriya ta samu baqi na nesa da suka shigo cikinta da zumman kasuwanci da cinikayya. Waxannan baqi na nesa da suka samu wannan martaba su ne Larabawa da Faransawa da Turawa sai kuma Asiyawa irin su Sinawa da suka shigo yanzu.

A hukumance, manhajar ilimi ta gida Nijeriya ta shigar da harsuna uku domin samun sauqin mu’amala da waxannan qasashe. Waxannan qasashe uku kuwa su ne Faransa da Ingilishi da Larabci. Dayake qasar Ingilishi ta raine mu (yayemu) sai hulxarmu ta fi qarfi da su mutanen Ingilishi. Hukumar ilimi ta qasa ba ta yi sakaci ba wajen tilasta harshen Ingilishi ya zama tilas a makarantunmu na gida ba. Yadda aka tilasta harshen Ingilishi ya kamata a tilasta na gida, domin hulxar da zumunta su qara qulluwa.

**Manazarta**

Adukola, T (2006). *Teaching and Learning in Nigeria’s Primary School*. Kaduna: National

Teachers Institute.

Banjo, A (2006). *Oxford Nigeria Dictionary*. Ibadan Oxford University Press in Association With University Press Plc.

Byrne, Huberty (1975). *The Teacher and His Pupils*. Oxford University Press London.

Coltall, S (1990). Developing Reading Strategies through Small Group Interaction. *RELC Journal* 212.55-69

Finnachiaro, M (1969). *Teaching English As A Second Language*. New York. Hamper and Row Publishers.

Federal Ministry of Education (2013) *National Policy on Education (6th Edition)*. Lagos: NERDC.

FME/NTI, Kaduna (2016). Sustainable Development Goals (SDGs Project) For Primary Schools Teachers. Kaduna: NTI.

Kroll, B (cd) (1990). *Second Language Writing Research Insight for Classroom*. New York Cambridge.

Olaofe, I.A (2013). *Teaching English in Second Language Context A Solution-Based Approach*. Zaria: Applied Language centre.

Rivers W.M and Temparly, M.S (1979). *A Practical Guide to Teaching English As A Second Foreign Language*. New York Oxford University Press.

Zarruq, R.M (1979). *Siffofin Aikin Koyarwa*. Oxford University London.